**[1]YUSUF Lawi, [2]ABDULLAHI Ramatu Maiyaki and [3]JAMILU Nura Musa**

[1]Department of Languages and Linguistics, University of Maiduguri, Borno State.
[2&3]Department of Hausa Language, College of Education Zing, Taraba State.

# Amfani da Azancin Magana wajen Yaƙin Neman Zaɓe a Siyasar Ƙaramar Hukumar Jalingo, Jihar Taraba

**Tsakure**

Wannan makala mai taken “Amfani da Azancin Magana wajen Yaƙin Neman Zaɓe a Siyasar Ƙaramar Hukumar Jalingo, Jihar Taraba” An gina ta ne kan abin da ya shafi azanci, wanda kuwa manufar aikin ita ce a zaƙulo ire-iren salalla na jan ra’ayi da ake amfani da su, da kuma bayani kan azanci waɗanda suke haɗe da karin magana, kirari, habaici, zambo da sauran ire-irensu da suke taimakawa wajen rinjayar ra’ayoyin jama’a. Binciken ya yi amfani da hanya mai inganci, inda aka tattara bayanai ta hanyar nazarin jawaban wasu 'yan siyasa a yaƙin neman zaɓe, tattaunawa da masu ruwa da tsaki, da kuma bibiyar saƙonnin siyasa a kafafen yaɗa labarai. An gudanar da binciken ne a ƙaramar hukumar Jalingo da ke jihar Taraba, wadda ke da muhimmiyar rawa a fagen siyasa da hulɗar jama’a. Sakamakon binciken ya nuna cewa maganganun azanci na taka muhimmiyar rawa wajen gina amincewa, tayar da sha’awa, da ƙarfafa goyon baya daga masu zaɓe. Haka kuma, an gano cewa nasarar yaƙin neman zaɓe na da alaƙa kai tsaye da yadda ɗan takara ke iya azanci cikin hikima da jan hankali. Binciken ya kammala da cewa azanci makamai ne masu tasiri a siyasa, musamman a matakin ƙaramar hukuma inda hulɗar kai tsaye da jama’a ke da ƙarfi. An ba da shawarar cewa ‘yan siyasa su riƙa amfani da azanci da aka yi amfani da su a cikin gaskiya da mutunci domin bunƙasa dimokuraɗiyya da haɗin kan al’umma.

**Muhimman Kalmomi:** Salon Jan Ra’ayi, Azanci, Yaƙin Neman Zaɓe, Siyasa.

**Received**: 10/04/2026 Accepted: 25/04/2026 08036115097, 08145067620
**Corresponding Author**: YUSUF, L. **Email**: andersonblessing44@gmail.com

**Article Citation**: Yusuf, L.; Abdullahi, R. M. and Jamilu, N. M. (2026). Amfani da Azancin Magana wajen Yaƙin Neman Zaɓe a Siyasar Ƙaramar Hukumar Jalingo, Jihar Taraba. *Jalingo Journal of Languages and Literary Studies (JAJ0LLS). 10 (1) pp.*
**Publishers**: Department of Languages and Linguistics, Taraba State University, Jalingo. **ISSN**: 2488-9067

## 1.0 Gabatarwa

Zaɓe muhimmiyar hanya ce ta tabbatar da dimokuraɗiyya a kowace al’umma. A tsarin siyasar Nijeriya, yaƙin neman zaɓe na taka rawar gani wajen isar da manufofi, jan hankalin masu kaɗa ƙuri’a, da kuma gina kyakkyawar alaƙa tsakanin ‘yan takara da jama’a. Yana daga cikin ɗabi’un

al’umma na cewa dokin mai baki ya fi gudu. Da haka ne kowa ke amfani da abin da ya sauwaƙa a gare shi, sai ya kambama shi a idon al’umma domin ya samu tudun dafawa. Inda suke amfani da wata dabara don burgewa ko don niyyar samun yardar wani, don ya amince da kai ko abin da kake faɗa. A irin wannan yanayi, akan yi amfani da azanci (hikima, dabara, da lafazi mai tasiri) waɗanda suke zama ginshiƙai masu muhimmanci wajen samun nasara. Azancin magana tushe ne na salon azanci, da wani fasihi ko fanni ya yi tasiri a kansa, ƙoƙarin zaƙulo ire-irensu kuma shi ne babbar manufar nazarin salo. Wannan aiki yana da masaniya game da kasancewar ɗan siyasa ya iya magana wajen jawo ra’ayin mabiyansa, ko kuma mafi shahara daga cikin al’umma wajen iya zance cikin hikima da zalaƙa. Don haka aikin ya taƙaita ne kan adabi, amma bai shafi dukkan ɓangarorin adabin ba, ya dubi ɓangaren azancin magana ne da ake amfani da su a fagen siyasa da 'yan takara a matakai daban-daban na kujerar shugabancin al’umma da yadda ake amfani da su a ƙaramar hukumar Jalingo, azancin magana da aka yi amfani da su a wannan aiki an same su ne ta: nazarin jawaban da ake yi a yaƙin neman zaɓe. da tattaunawa da wasu ‘yan takara, magoya baya, da masu zaɓe. da kuma bibiyar tallace-tallacen siyasa a kafafen yaɗa labarai da tarukan gangami da allunan tallace-tallace na 'yan siyasa.

## 1.1 Azancin Magana

Azancin magana yana nuna iya laƙantar harshe ne na mai yin magana kuma ya sanya mai sauraro rashin ƙosawa da son jin labarai da ake yi masa komin yawansu. A zamanin da, samari da ‘yan mata sukan nuna soyayyarsu ta hanyar nuna ƙwarewa a azancin magana har ma ya kasance duk budurwa da ta ƙware wajen azancin magana tana samun tagomashi wajen samari. Mata da ‘yan Daudu su suka fi yin amfani da azancin magana. A haƙiƙanin gaskiya duk hmutum da bai fiya amfani da azancin magana, to maganarsa lam ice a ko-da-yaushe. Dangane da haka ne masana irin su:

Ɗangambo (1984), ya bayyana kalmar azanci da nuna adon magana, inda ya ce, “Wasu maganganun hikima ne guntaye da akan samu masu kama da karin magana. Wato zance ne a dunƙule wanda yake cike da hikima.”

Ɗanhausa (2012) ya ce "Azancin magana gajerun jimloli ne waɗanda ba safai ma'anarsu ta zahiri ke nuna abin da suke nufi ba.” Wannan na nufin a karin magana a kan sakaya abin da ake nufi ta hanyar amfani da hikima na zantuka.

Faragai (2008) ya bayyana cewa "Su irin waɗannan zantukan magana sun samo asali ne lokacin da Bahaushe ya fara yin farauta yana kama namun daji, idan wani mutum ya yi ƙoƙari ya kama dabba ko ya kashe ta a wajen wannan yunƙuri na bajinta yakan faɗi wasu lafuzza na maganganu na kuranta kai waɗanda suka ƙunshi hikimomi da kalmomi da suka yi kama da karin magana.” Haka kuma ana hasashen karin magana sun samo asali ne daga taken kirari saboda take da kirari kusan a ce sun riga karin magana wanzuwa, tun da Bahaushe farauta ya fara yi kafin sauran sana'o'I suka biyo bayanta. Wasu masana na cewa, ta zo ne ta hanyar ɗabi'u da al'adun Hausawa. (Ɗanyaya 2018).

### 1.1.1 Ire-iren Azancin magana

Azancin magana na nufin hikima da fasaha wajen amfani da harshe domin isar da saƙo cikin taƙaitawa, jan hankali da tasiri. A al’adar Hausawa, azanci ya zama ginshiƙi wajen sadarwa, musamman a wa’azi da waƙa da siyasa da zaman yau da kullum. Ga manyan ire-irensa:

a) Karin Magana
b) Kirari
c) Habaici

d) Zambo
e) Ba’a
f) Almara da sauransu. (Faragai 2008).

## 1.2 Ma'anar Siyasa

Ba tare da yin dogon bayani ba kalmar siyasa aro ta aka yi daga harshen Larabci wato, “*Assiyasat*” amma idan aka dubi ma’anar da Larabawa suka ba wa kalmar ita ce: “Hanyar mulki da kuma hanyar sarrafa tunanin mutane domin shugabantarsu, (Mukhtar, 2020:30). Babban kundin nan na Ƙamasun Larabci (1987) mai suna *Lisanul Arab* ya nuna kalmar siyasa a matsayin tafiyar da abu ta hanyar da zai yi daidai da abin. Ya ƙara da cewa har ma idan aka ga mutum ya tsaya a kan dabbobi, kuma sun yarda da shi sai a ce wane ya siyasance dabbobin, ko kuma a ce shugaba ya siyasance talaƙawansa in an ji suna zaune lafiya.

A ƙamasun *Almunjid-Abjadi* (1998) an nuna siyasa na da ma’ana guda biyu. Ta farko dai, siyasa na nufin ingantar da al’umma da shiryar da su zuwa ga hanyar tsira, ko a kusa ko a nesa. Ma’ana ta biyu ita ce, siyasa na nufin gudanar da fannin mulki da ayyukan ƙasa a cikin ƙasar ko a wajenta, ta haka ake samin siyasar harkokin cikin gida da siyasar harkokin ƙasashen waje.

Ƙamusoshin Hausa da masana Harshen Hausa da dama sun ba da ma’anar siyasa. Waɗannan masana ko litattatafai sun haɗa da Bargery (1934) da Abraham (1962) da Lawal (1983) da Faragai (1984) da Ƙamasun Hausa (2006). Bargery (1934) yana cewa siyasa tana nufin rangwame farashin kowane abu kuma a tausasawa a cikin al’amura. Wannan ra’ayi ya yi daidai da na Abraham (1962). A cikin Ƙamasun Hausa (1992) na Jami’ar Bayero ta Kano kuwa an kawo ma’anonin siyasa har guda huɗu da suka haɗa da:

i. Tafiyar da al’amuran jama’a ta hanyar neman ra’ayinsu da shawarwari da su.
ii. Rangwame musanman a ciniki.
iii. Da kuma ma’anar siyasa da ke cewa, dabara ce ko wayo.
iv. Da kuma ma’anar siyasa ta iya hulɗa da jama’a.

Waɗannan ra’ayoyi sun sha bamban da na Lawal (2019). Domin shi cewa ya yi, “Siyasa tana nufin halayyar cim ma wani buri dangane da mutane ko kuma gwamnati.” Shi kuwa Faragai (2021) ya yi tsokaci a kan ma’anonin siyasa har guda biyu inda yake cewa: Ma’ana ta farko ita ce; siyasa tana nufin gudanar da mulki da tafiyar da mulkin jama’a ta ba wa kowa hakkinsa. Ma’ana ta biyu kuwa ita ce; a wajen Bahaushe idan ya ce ya yi min siyasa yana nufin: -Yaudara ko dabara –sauƙi ko rangwame - lumana ko lallami.

Abubakar (2019, sh. 53), Siyasa lamari ne da yake shafar mas'alar ƙarfi da iko da tafiyar da lamurran al'umma, don haka sha'ani ne wanda yake ɗauke da ma’anoni masu muhimmanci a cikin al'umma da suka shafi: zaɓe da ƙwace mulki da tafiyar da mulki da ikon ƙasa da zartarwa da juyin mulki da yin juyin-juya-hali da tabbata kan mulki da canjin shugaba ko jagora da makamantansu. Sa’id (2022, sh. 172), Siyasa wata hanya ce ta gudanar da zaɓaɓɓiyar gwamnati ta hanyar Dimokuraɗiyya a ƙarƙashin tsarin mulkin ƙasa, inda za a zaɓi shugabanni masu tafiyar da ita a ƙarƙashin kafaffun jama’iyyu. Ta wata fuskar kuma, siyasa tana iya ba da ma’anar ƙwarewa wajen iya tafiyar da jama’a da jure wa duk wata matsala ta su (Ɗahiru, 2020).

A taƙaice dai za mu iya cewa siyasa tana nufin hanyar shugabantar al'umma. Wannan ita ce ma'anar siyasa ta zahiri. Ko hanya ce da jama'a ke bi wajen samun damar zaɓen shugaba da kansu, waɗanda suke ganin zai jagorance su da ƙwato masu 'yanci da kuma samun damar faɗin albarkacin bakinsu.

## 1.3 Hanyar gudanar da bincike

Wannan bincike an gudanar da shi ne ta hanyar bin matakai na ilimi domin tattara sahihan bayanai da nazarinsu cikin tsari. An yi amfani da hanya mai inganci wanda yake ba da dama wajen fahimtar ma'ana da salo da hikimomin da ke cikin jawaban yaƙin neman zaɓe. Wannan hanya ta dace da nazarin harshe da azanci, ba tare da mayar da hankali kan lissafi ko ƙididdiga ba. An tattara bayanai ta hanyar nazarin rubutattun jawaban yaƙin neman zaɓe da duba fastoci da takardun tallatawa da saƙonnin siyasa da kuma bibiyar bayanai daga kafafen yaɗa labarai (rediyo da talabijin da shafukan sada zumunta). An kuma tattauna da wasu 'yan takara da wakilansu da magoya baya da masu zaɓe da kuma jin ra'ayin malamai ko masu ruwa da tsaki a fagen siyasa, sai kuma halartar tarukan gangamin yaƙin neman zaɓe. An zaɓi mahalarta ne ta hanyar zaɓen mutanen da suke da alaƙa kai tsaye da batun binciken, kamar: 'Yan siyasa da masu kamfen da kuma masu zaɓe. An yi amfani da hanyar nazarin zance domin: Gano sigogin salon jan ra'ayi da tantance ire-iren azanci da aka yi amfani da su (karin magana, kirari, habaici, zambo da sauransu) da kuma fahimtar tasirin su ga masu sauraro. An fitar da misalai daga jawaban, sannan aka yi sharhi a kansu domin nuna ma'anarsu da tasirinsu.

## 2.0 Amfani da Azancin magana wajen yaƙin neman Zaɓe a Siyasar Ƙaramar Hukumar Jalingo, Jihar Taraba

Wannan ya ƙunshi kawo wasu azancin magana ne da irin rawar da suke takawa cikin tsari waɗanda 'yan siyasa ke amfani da su wajen yaƙin neman zaɓe a kujeru mabambanta na shugabancin al'umma a ƙaramar humar Jalingo da suke zuwa a sigogi na musamman. Wajen zayyano waɗannan azancin, an yi la'akari da rukunan masu amfani da irin waɗannan azancin da suka haɗa da: cikin zantukan 'yan takara yayin yaƙin neman zaɓe, daga bakin wasu mutane masu tallata 'yan takara yayin yaƙin neman zaɓe da cikin fostocin 'yan takara da kuma cikin wasu waƙoƙin 'yan takara daga bakin mawaƙa.

### 2.1 Ƙalailaice bayanin yadda 'yan siyasa ke amfani da azancin magana wajen yaƙin neman zaɓe

Yana daga cikin ɗabi'un al'umma na cewa dokin mai baki ya fi gudu. Da haka ne kowa ke amfani da abin da ya sawwaƙa a gare shi, sai ya kambama ta a idon al'umma domin ya samu tudun dafawa. Al'umma a kullum suna neman hanyar da za su dogara da ita ne wajen al'amurar rayuwarsu, musamman idan aka zo fagen siyasa wajen neman shugaba da zai jagorance su domin su samu ingancin rayuwa da ɗorewar zaman lafiya.

To, dangane da haka a cikin al'umma musammam 'yan takara da masu tallata su akan samu sun keɓantu da irin waɗannan maganganun azanci wajen yaƙin neman zaɓe a kujeru mabambanta kama daga Shuwagabanin ƙasa da Gwamnonin Jiha da na Majalisar Dattawa da Majilasar Wakilai da Shugabannin Ƙanana Hukumomi da kuma kujerun kansila. Kamar yadda aka bayyana a baya waɗannan shugabannin musamman, idan sun ziyarci mutanen sukan cusa masu waɗannan zantuka na azancin magana domin jawo ra'ayoyinsu.

To daga cikin waɗannan, ‘yan siyasa da masu gabatar da 'yan takara da kuma mawaƙansu kan yi amfani da karin magana da yabo da kirari wajen yaƙin neman zaɓe. Amma idan sun ci zabe sai su canja zance ko su manta da al’umma. Don haka, dangane da wannan aiki da farko an zayanno irin waɗannan azancin maganan da tsarin da suke cikin waɗannan rukunan al’umma ke amfani da su, sannan a yi sharhi kan kowanne daga cikinsu.

**“Aski ya zo gaban goshi”**

’Yan siyasa kan yi amfani da wannan domin nuna cewa lokaci zaɓe ya ƙarato. Ma’ana a siyasa: *Lokacin zaɓe ya yi, dole ne a ɗauki mataki.*

**“Bakin da ba ya kure maye ne”**

Ana amfani da shi wajen sukar shugabannin da ba sa magana ko kare muradun jama’a. Saƙo: *Shugaba dole ne ya zama mai faɗin gaskiya da kare haƙƙin jama’a.*

**“Da ɗan gari akan ci gari”**

Ana amfani da shi wajen ƙarfafa zaɓen ɗan asalin yankin. Saƙo: *Ku zaɓi ɗan gida domin shi ya fi sanin matsalolinku.*

**“Da kaɗan-kaɗan matankaɗi kan shiga gora”**

Ana amfani da shi wajen nuna cewa ci gaba na zuwa ne a hankali. Saƙo: *Ko da mun fara da ƙanana, za mu kai ga babba.*

**“Da kai da kaya duk mallakar wuya ce”**

Ana amfani da shi wajen nuna cewa shugabanci nauyi ne mai wahala. Saƙo: *Mu shirye muke mu ɗauki wannan nauyi domin ku.*

**“Dambu in ya yi yawa ba ya jin mai”**

Ana amfani da shi wajen sukar yawan alƙawura marasa tasiri. Saƙo: *Ba yawa ake bukata ba, inganci ake so.*

**“Ɗan ƙwarai azurfan dangi”**

Ana amfani da shi wajen yabon ɗan takara. Saƙo: *Wannan ɗan takara abin alfahari ne ga al’umma.*

**“Hannu da yayawa maganin ƙazamar miya”**

Ana amfani da shi wajen nuna buƙatar haɗin kai. Saƙo: *Sai mun haɗa kai za mu magance matsalolinmu.*

**“Hannu ɗaya ba ya ɗaukan jinka”**

Wannan na nuni da muhimmancin aiki tare. Saƙo: *Ku ba mu goyon baya domin mu yi aiki tare.*

**“Mun gaji da gafara sa ba mu ga ƙaho ba”**

Ana amfani da shi wajen nuna gajiya da alƙawuran banza. Saƙo: *Mun gaji da maganganu, muna son aiki a zahiri.*

**“Mun gaji da tura mota ta bule mu da hayaƙi”**

Ana amfani da shi wajen sukar shugabanci mara amfani. Saƙo: *Mun gaji da wahala ba tare da cin moriya ba.*

**"Saniya ba ta gazawa da ƙahonta"**

Ana amfani da shi wajen nuna cewa shugaba mai ƙwarewa yana da dabarunsa. Saƙo: *Muna da ƙwarewa da za mu warware matsaloli.*

**"Sayen na gari mai da kuɗi gida"**

Ana amfani da shi wajen ƙarfafa tattalin arzikin gida da zaɓen ɗan yankin. Saƙo: *Ku zaɓi namu domin ribar ta zauna a yankinmu.*

An raba waɗannan azancin magana kamar

i. Cikin maganganun 'yan takara yayin yaƙin neman zaɓe,
ii. Daga bakin wasu mutane masu tallata 'yan takara a lokacin yaƙin neman zaɓe
iii. Cikin fostocin yantakara
iv. Cikin wasu waƙoƙin 'yan takara daga baƙin mawaƙa

### 2.1.1 Cikin maganganun 'yan takara yayin yaƙin neman zaɓe

Kamar yadda yake cikin tsarin neman kujerar shugabancin al'umma a wannan ƙasa, 'yan takara kan ziyarci al'umma a wurare daban-daban ko dai a gidajensu da wajen majalasinsu da ofisoshinsu. To, a irin waɗannan wuraren 'yan takara da kansu kan yi amfani da wasu kalmomin azanci da zalaka don burgewa don jawo hankalin mutanen domin su saci zuciyarsu su kuma amince da su a lokacin zaɓe su jefa masu kur'ia don su samu nasara. To irin waɗannan azancin magana sun haɗa da:

***v.Ta hanyar kushe abokan takararsu na kujerar da suke nema***

Misali akwai wani lokaci da ɗan takarar gwamnan Jihar Taraba na jam'iyar APC 2019 wato Sen. Sani Abubakar Ɗanladi da tawagarsa lokacin da suka je yaƙin neman zaɓe na kujerar gwamna a wasu mazaɓu a cikin garin Jalingo sun yi amfani da azancin magana kamar haka:

- *"mu muka ɗaure kura kuma mu za mu kwance ta"*
- *"ƙwace goruba a hannun kuturu ba wahala"*
- *"hannun karɓa hannun mayarwa"*

Ga sharhin waɗannan azancin magana da Ahmed Yusuf Gamaliya (Shugaban tawagar yaƙin neman zaɓen) ɗan takarar gomna na APC a 2019 wato Sani Abubakar Ɗanladi lokacin da suka je yaƙin neman zaɓe a cikin garin Jalingo inda yake cewa. Sharhi na farko inda yake cewa:

**"mu muka ɗaure kura kuma mu za mu kwance ta"**

*Ma'ana (mu muka kawo gwamna mai ci kuma mu muka san yadda za mu kawar da shi a kujerar) jama'a suka yi ihu da farin ciki domin suna ganin maganarsa ta kama zuciyarsu domin su suka kawo gwamna mai ci kuma su suka san yadda za su kawar da shi a kujerar da irin dabarar da su ka yi suka kawo shi.*

Ya ci gaba da bayani inda ya sake cewa

**"ƙwace goruba a hannun kutura ba zai yi wuya ba"**

*ma'ana (tunda su suka kawo shi a gwamnan to kuwa karɓar mulki a hannunsa ba zai masu wahala ba matuƙar jama'a a lokacin zaɓe sun kaɗa masu ƙuri'a).*

Haka ya ci gaba da magana har lokacin da ɗan takarar gwamnan ya karɓi maganar. Shi ma kuma lokacin da Sani Abubakar Ɗanladi na APC a 2019 ya yi bayaninsa ya jaddada hakan. kuma jama’a sun tabbatar masu da cewa za su yi iya ƙoƙarinsu wajen ba su ƙuri’arsu domin su kawo masu cigaba. Wannan shi ne kaɗan daga cikin misalan azancin magana da ‘yan siyasa suka yi amfani da su kenan wajen yaƙin neman zaɓe a ƙaramar hukumar Jalingo.

**2.1.2 Daga bakin wasu mutane masu tallata 'yan takara lokacin yaƙin neman zaɓe**

Ta hanyar bayyana ko zayyano wasu ayyuka da suka yi a baya

Ta hanyar zayyano wasu ayyuka da za su yi a gaba in suka samu nasara

vi. **Ta hanyar faɗar wasu ayyukansu na alheri da suka yi a baya**

Sau da dama wasu mutane masu tallata 'yan takara kan yi amfani da wasu azancin magana domin tallata 'yan takararsu yayin da suke fadar wasu ayyuka na alheri da 'yan takarar suka yi a wurare daban-daban. Misali ɗan takarar kujerar ɗan Majalisar Tarayya mai Wakiltar Jalingo da Yorro da Zing wato Isma’ila Yusha’u Maihanci. Akwai wasu azanci da mutanensa suka yi amfani da su wajen yaƙin neman zaɓensa a unguwanin cikin Jalingo, misalan azancin sun haɗa da:

- *namu ba irin nasu ba ne ba.*
- *mu gani a ƙasa wai an ce da kare ana biki a gidanku.*

Dangane da waɗannan azancin magana, akwai ayyuka ne da shi ɗan takarar ya yi wanda sauran 'yan takarar ba su yi ba, misali. Shi Maihanchi ya ba wa wasu matasa ayyukan yi na gwamnati a ɓangarori daban-daban cikin fadar jiha kamar a kwalejin ilmi ta Zing da kwalejin noma ta Jalingo da Jami’ar Jihar Taraba da wasu Hukumomi a cikin Jihar. To, da waɗannan ne ya sa masu tallata shi suke amfani da irin wannan azanci na cewa *namu ba irin nasu ba ne ba.* wato shi nasu ya yi amma nasu ba su yi hakan ba.

Haka kuma, duk da cewa shi ɗan takarar bai riƙe wani mukamin gwamnati ba ko kuma ba ya kan kujera na shugabanci, amma ya yi wasu ayyuka da mutane za su gani a bayyane da idonsu ba sai wani ya gaya masu ba, kuma ba ya alkawarin zai yi masu abu sai dai kawai su gani ya yi, da wannan ne masu tallata shi suke amfani da wannan azancin magana na cewa ‘*mu gani a ƙasa wai an ce da kare ana biki a gidanku’.*

**2.1.3 Cikin wasu 'yan takara da bakin mawaƙa a cikin waƙoƙinsu**

vii. Salon kwantar da harshe ko daɗin baki

viii. Yabo daga wasu halayyarsu na kirki

ix. Salon jan ra’ayi

**2.1.3-1 Salon kwantar da harshe ko daɗin baki**

Wannan salo na kwantar da harshe ko daɗin baki a kan yi amfani da kalmomi masu nuna girmamawa, tausayi da kulawa ga al’umma. Wato a faɗa wa wani magana mai faranta masa rai domin samun wata biyan buƙata daga gare shi. ko da kuwa maganar ba gaskiya ce aka faɗa masa ba. ’Yan siyasa kan yi amfani da kalmomi masu nuna girmamawa, tausayi da kulawa ga al’umma. Misali irin su:

x. Wuya!

xi. Farin mutum farin aniya

xii. Ko da naka ka so na ƙwarai

xiii. Daram dam-dam
xiv. Huɗu sau biyu
xv. Balbela ba ki yi farin banza ba.

**Misalai a jawaban yaƙin neman zaɓe:**

- *"'Yan'uwa na Jalingo, ku ne ginshiƙin cigaban wannan gari. Duk abin da za mu yi domin inganta rayuwarku ne."*
- *"Muna jin ƙorafinku, kuma muna tare da ku a kowane hali."*
- *"Ku kwantar da hankalinku, idan kuka ba mu dama za mu kawo sauyi mai amfani ga kowa."*

A nan ana amfani da kalmomi masu laushi domin ƙara kusantar jama'a.

**2.1.3-2 Yabo daga wasu halayyarsu na kirki**

A wannan salo, ɗan siyasa ko masu kamfensa kan ambaci wasu kyawawan halaye ko ayyukan alheri da ya taɓa yi domin su nuna cewa ya cancanci a zaɓe shi.

**Misalai:**

- *"Wannan mutum kun san shi, tun kafin ya shiga siyasa yana taimakon marasa ƙarfi a cikin al'umma."*
- *"Shi mutum ne mai gaskiya da riƙon amana, shi ya sa muka ga ya dace ya jagorance mu."*
- *"Ku tuna lokacin da ya gina rijiyar ruwa a wannan unguwa ba tare da wani ya tilasta masa ba."*

Wannan yabo yana ƙara gina amincewa tsakanin ɗan takara da jama'a.

**2.1.3.3 Salon jan ra'ayi**

Salon jan ra'ayi wasu dabaru ne da ake shimfiɗawa wajen jayo hankalin al'umma a fagen siyasa. Akan yi haka ne domin su aminta da saƙon da ake son a isar masu domin su ba da goyon baya a bisa ƙashin kansu. Irin wannan salo yana zuwa ta fuskoki daban-daban. Misali akan kafa hujja da wasu irin ayyuka da aka gudanar don su zama dalili na ƙara goyon baya. Akan kuma nuna wa mutane damuwa da ake ciki na rashin cigaba da rashin kulawa da aka yi wa talakawa da kuma aibun zaɓen tumun dare. Haka kuma akan fito da kyawawan abubuwa tattare da wanda ake so. Kuma akan bayyana manufofi ko kuma a iya kwatance tsakanin abubuwa guda biyu.

**Misalai:**

i. *"Ku zaɓi canji domin 'ya'yanmu su samu makoma mai kyau."*
ii. *"Idan muka haɗa kai muka zaɓi wannan jam'iyya, za mu samu hanyoyi, makarantu da asibitoci."*
iii. *"Hannu ɗaya ba ya ɗaukar jinka; sai mun haɗa kai za mu kawo cigaba a Jalingo."*

A nan ana amfani da kalmomi da misalai da ke ƙarfafa mutane su yanke shawara ta goyon bayan ɗan takara.

Ga wani misali daga ciki wanda tsohon mataimakin gwamnan na jihar Taraba Sani Abubakar Danladi a 2015 a jawabinsa a garin Jalingo, lokacin yaƙin neman zaɓen ɗan takarar shugaban ƙasa Goodluck Jonathan da na ɗan takarar gwamnan jihar Taraba Arc. Darius Dickson Ishaku a ƙarƙashin jam'iyyar PDP inda yake cewa:

> "*mun zo biyan bashi. Ga Goodluck Jonathan ga Darius Dickson, kyawun ɗa ya mai da ragon sunansa. Bayan hanyar motar da aka samar maku ga asibiti nan, ga masallaci. Duk ɗan gida wanda bai zamo agola ba, ga Goodluck Jonathan ga Darius Dickson, wanda al'ummar ƙasar nan suka ce 'sai ka yi'*".

Idan muka duba a nan, wannan ɗan siyasa ya nuna wa mutane cewa babu wani abu da mutane za su saka masu da shi dangane da irin ayyuka da suka yi masu, face su ba su ƙuri'arsu, a lokacin gudanar da zaɓe. saboda haka a siyasa ana aiwatar da irin waɗannan ne ta hanyar amfani da harshe wajen magana mai daɗi ko tunatarwa ko kuma jawo hankali da bayyana manufofi ko tona gaskiyar abu.

## 3.0 Abubuwan da bincike ya gano

Bayan an yi nazarin azancin magana da 'yan siyasa ke amfani da su wajen yaƙin neman zaɓe, daga cikin abubuwan da aka samu nasarar ganowa:

i. An gano irin maganganun azanci da 'yan siyasa ke amfani da su wajen yaƙin neman zaɓe.
ii. 'Yan siyasa kan yi amfani da salon jan ra'ayi wajen kafa hujja da wasu irin ayyuka da aka gudanar don su zama dalili na ƙara goyon baya.

## 4.0 Kammalawa

Wannan bincike mai taken **"**Amfani da Azancin Magana wajen Yaƙin Neman Zaɓe a Siyasar Ƙaramar Hukumar Jalingo, Jihar Taraba**"** ya yi nazari kan yadda 'yan siyasa ke amfani da azanci domin rinjayar ra'ayin masu zaɓe. An gudanar da binciken ne a Jalingo Jihar Taraba. Binciken ya nuna cewa azancin magana kamar karin magana, kirari, habaici, zambo, suna taka muhimmiyar rawa wajen isar da saƙon siyasa ga jama'a. 'Yan siyasa kan yi amfani da waɗannan salo domin su jawo hankalin jama'a, su ƙarfafa goyon baya, kuma su soki abokan hamayya cikin hikima. Haka kuma binciken ya nuna cewa amfani da azanci yana sauƙaƙa fahimtar saƙon siyasa ga jama'a saboda irin waɗannan maganganu suna da alaƙa da al'ada da rayuwar yau da kullum ta al'umma. Wannan yana sa jawaban yaƙin neman zaɓe su zama masu armashi da tasiri ga masu sauraro.

## 5.0 Shawarwari

i. Ya kamata 'yan siyasa su riƙa amfani da azanci cikin hikima da gaskiya, ba tare da amfani da shi wajen yaudara ko ɓata suna ko tayar da rikici a tsakanin al'umma ba.
ii. Masu bincike su ƙara zurfafa nazari kan dangantakar da ke tsakanin harshe da siyasa, musamman a matakin ƙaramar hukuma.
iii. Ya kamata masu zaɓe su riƙa lura da saƙonnin siyasa sosai, su bambanta tsakanin maganganun jan hankali da ainihin ayyukan da za su amfani al'umma.
iv. Ya kamata gwamnati ta ƙarfafa ilimin siyasa da wayar da kan jama'a domin su fahimci yadda ake amfani da dabarun magana a yaƙin neman zaɓe.

## Manazarta


Abubakar, U.M (2019) Nazarin Turken Siyasa a wasu Waƙoƙin Makaɗi Ibrahim Ibrahim: Kano. Takardar da aka gabatar domin cikasa ƙa'idar neman neman digiri na biyu a fannin adabin Hausa, a sashen koyar da harsunan Najeriya, jami'ar Bayaero.

Aliyu, H.G. (2019). Tasirin Maganganun Azanci a Littafin *Amon 'Yanci Da Na Bakin Kishi da Na 'Yar Tsana*). Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Bayero kano.

Bunza, A.M (2005) "Arashi shi gogi Baƙauye: Nazarin Karin Magana" Sakkwato: Takardar Da Aka Gabatar A Taron Ƙara Wa Juna Sani, Sashen Koyar Da Harsunan Najeriya, Jami'an Usmanu Ɗanfodiyo, Sakkwato.

Bunza, A.M (2006) "Cultural Shortcoming In Hausa Popular Proverbs", Ille- Ife: Taron Ƙara Wa Juna Sani Kan Karin Magana, Jami'ar Obafemi Awolowo.

Ɗahiru, Y. (2020) Nazarin wasu Maganganun Azanci a Waƙoƙin Siyasa na Shalelen Mawaƙan Bauchi: Kano. Takardar da aka gabatar domin cikasa ƙa'idar neman neman digiri na biyu a a fannin adabin Hausa, a sashen koyar da harsunan Najeriya, jami'ar Bayaero.

Ɗan Hausa, A. M. (2012). Hausa Mai Dubun Hikima. Kano; Century Research and Publishing Company.

Ɗanyaya, B.M. (2007) Karin Maganar Hausawa.Sokoto: Makarantar Hausa.

Diso, A.H. (1997). (Zambo Da Yabo A Matsayin Dabarun Jawo Hankali A rubutattun Wakokin Hausa). Kundin Digiri Na Biyu, Jami'ar Bayero Kano.

Dunfawa, A. A. (2005). "Zambo Da Habaici a Wakokin Addini". Journal of Hausa Studies ɓol. I no. 2, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Sokoto Usmanu Danfodiyo Uniɓersiy.

Faragai, N.A. (2018). (Nazarin Sigogin Adon Harshe A Wakokin Hafiz Abdallah). Kundin Digiri Na Biyu, Jamilar Bayero Kano.

Koko.H.S. (2011) *Hausa Cikin Hausa.Sakkwato*: Sashen Nazarin Harsunan Najeriya Kwalejin Ilimi Ta Shehu Shagari, Sakkwato Najeriya.

Lawan, S. (2021) Nazarin Wasu Sassan Maganganun Azanci cikin Shirin Duniya Makaranta na Gidan Rediyon Jihar Zamfara: Kano. Takardar da aka gabatar domin cikasa ƙa'idar neman neman digiri na biyu a Fannin nazarin Hausa, a Sashen Koyar da Harsunan Najeriya, Jami'ar Bayaero.

Mainasara, A. (2021) Tarsashin Wasu Sassan Maganganun Azanci a Zubin Waƙoƙin Malam Abubakar Ibrahim Kantama: Kano. Takardar da aka gabatar domin cikasa ƙa'idar binciken samun digiri na uku a fannin adabin Hausa, a sashen koyar da harsunan Najeriya, jami'ar Bayaero.

Zainab, I. (2011)" Gaskiya A Adabin Bahaushe: Nazari A Karin Magana". Katsina: Takardar Da Aka Gabatar A Taron Ƙara wa Juna Sani, Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, Jami'ar Umaru Musa 'Yar'adua.

Zarruk da sauransu (1986) *Sabuwar hanyar nazarin Hausa.Don ƙananan makarantun Sakandare, na ɗaya (1)*, Uniɓersiy Press PLC Ibadan